**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.15 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Wando Sai Da Zariya: Kimar Namiji A Wajen Mace A Mahangar Kassu Zurmi

[1]**Ibrahim Abdullahi Sarki Sudan,**
[2]**Nura Lawal**

[1]Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sokoto
[2]Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano

**Corresponding Author: Ibrahim Abdullahi Sarki Sudan** ibrasskg@gmail.com
Phone 08036153050

**Tsakure**

Babbar manufar wannan takarda ita ce fito da yanayin dangantakar mata da maza, wato 'yantauri da mafarauta da makamantansu a wasu waƙoƙin Kassu Zurmi, musamman ta la'akari da tsarin zamantakewar alaƙar maza da mata tun daga matakin 'yanmatanci da samartaka har zuwa zamantakewar aure. Hanyoyin da aka yi amfani da su a wajen tattaro bayanai da misalan ɗiyan waƙoƙin da aka yi amfani da su, sun haɗa da sauraren wasu waƙoƙin daga MP3 sannan aka juyar da su a rubuce. Haka kuma an tsamo wasu ɗiyan waƙoƙin daga littattafai masu ɗauke da waƙoƙin Kassu Zurmi. A wannan nazari an lura, Kassu Zurmi yana amfani da dabarun na bibiyar yanayin dangantakar soyayyar da take tsakanin jarumansa da kuma mata duk da cewa yawancin 'yantauri da mafarauta duk matalauta ne ko kuma matsiyata kamar yadda yake ambatar su a cikin waƙoƙinsa. Har wa yau, an fahimci a wasu waƙoƙin na Kassu Zurmi, yakan nuna yadda kyakkyawar alaƙa take tsakanin mata da maza, musamman ta fuskar yadda 'yanmata da mata suke nuna gabata da hakin kyauta da rufa asiri da bayar da shawarwari da kuma taimako ga mazajen duk da yanayinsu na fatara. A waƙoƙin na Kassu, an gano cewa, mata suna son mazaje jarumai ko da kuwa ba su da arziki, don shahara ko bajintarsu ko kuma surar jikinsu. Ashe kenan, akwai kyakkyawar alaƙa ta soyayya tsakanin mata da maza jarumai ta hanyar yin haƙuri da yanayinsu na ɗauko magana da kuma rashin yin katabus a ɓangaren hidima, musamman wadda ta shafi kuɗi. Nazarin ya yi ƙoƙarin tabbatar da cewa, waƙoƙin Kassu, waƙoƙi ne da suka yi la'akari da matsayin zamantakewar mace da namiji da tabbatar da tunanin mace ba ta iya yi sai da namiji komai lalacewarsa kamar dai yadda wando ba ya tabbata a ƙugu sai da zariya.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Waƙoƙin baka na Hausa, waƙoƙi ne da suke tafiya tare da tsarin zamantakewar al'ummar ta Hausawa. Hakan ya ba Kassu Zurmi damar zama makaɗin jaruntaka, wato makaɗin maza kamar mafarauta da 'yantauri da kuma ɓarayi. Waƙoƙin Kassu sun fito da yanayin dangantakar maza, wato mafarauta da 'yantauri da kuma ɓarayi da iyalinsu da kuma sauran jama'a ta la'akari da ɗabi'un al'umma. Kassu ya gina waƙoƙin ta la'akari da abubuwan da suke wakana a cikin al'umma da kuma abubuwan da suke kewaye da su. Masana da manazarta adabi da al'adun Hausawa irin su Sulaiman (1983) Gusau (2008 da 2011 da 2023) da Yahya (1997) da Bunza (2009 da 2014) da Magaji ( 1980 da 2016) da Funtua (2015) da Usman (2011) da Kaura (2017) da Lawal da Tahir (2025) da sauransu sun yi tsokaci dangane da yadda waƙar baka ta wanzu da kuma ginuwarta a tsakanin al'ummar Hausawa da kuma samar da wasu matakan nazarin waƙoƙin. Haka kuma, wasu masana da manazarta sun yi nazari da sharhi dangane da wasu ɓangarori na zamantakewar al'ummar Hausawa. Sai dai masanan da manazartan ba su waiwayi wajibcin namiji a rayuwar matan Hausawa kamar yadda Kassu ya kawo a waƙoƙinsa ba.

Waƙoƙin maza, waƙoƙi ne da makaɗan maza suke yi wa mutane masu nuna jarunta ko bajinta, kamar mayaƙa da mafarauta da 'yantauri da 'yandambe da makamantansu. A irin waɗannan waƙoƙin akan yi yabo ko zuga ga gwarzayen saboda ƙarfinsu da jaruntaka ko rashin tsoronsu (Ɗangambo,2011:46-47). Kassu Zurmi yana ɗaya daga cikin shahararrun makaɗan maza a zamaninsa wanda ya yi ƙoƙari wajen fito da asali da halaye da ɗabi'un da kuma yanayin zamantakewar gwarzayensa a waƙoƙin nasa. Zamantakewa na nufin yanayin zaman tare a tsakanin mata da maza ko iyaye da iyalansu ko zaman yau da kullum a tsakanin al'umma dangane da auratayya da maƙwabtaka da zaman gari ɗaya ko al'umma ɗaya (Ingawa, 2012, Sh.41). Haka kuma, zamantakewa na iya ƙunsar yadda al'umma take gudanar da harkokin rayuwarta na yau da kullum, kuma kowace al'umma tana da tsarin yadda take gudanar da harkokin rayuwarta da ta bambanta da na wata (Inuwa, 2009, Sh.137). Ashe ke nan, a irin wannan tsarin zama ne, Hausawa sukan yi la'akari da yanayin alaƙar da take a tsakanin maza da mata a kowane mataki ko yanayin, wato tun daga yarinta zuwa zaman aure da iyali. Tunanin mutane da yawa a kan Kassu shi ne ya zuga ko ya yaba maza a kan abin da suka sa a gaba. Kasancewar waƙoƙin nasa hoto ne na rayuwa, dole a hango tsattsafin wannan lamari na irin kulawar da maza suke samu a wajen matan da suke tare da su. Wannan yanayi da aka yi nazari ya nuna cewa, duk halin da namiji ya tsinci kansa na lalacewa, ba za a rasa macen da ya zama mata wajibi ta kula da shi ba.

### 1.1 Taƙaitaccen Tarihin Makaɗa Kassu Zurmi

An haifi Alhaji Abubakar Kassu Zurmi ne a shekarar 1923 a garin Magarya ta ƙasar Zurmi, kuma a ƙaramar hukumar Zurmi, a jihar Zamfara ta yanzu. Makaɗin ya sami wannan suna ne (na Kassu) daga laƙabin *MaiKassuwa,* wanda aka gutsure ya koma "Kassu". Wai mahaifiyarsa ta haife shi ne a ranar kasuwar Dunfawa bayan ta dawo daga cin kasuwa (Kaura 2017:13)

Kassu ya gaji kiɗa ne a wajen mahaifinsa Muhammadu Ganga, wanda makaɗin farauta ne. Tun da Kassu Zurmi ya tasa, ya fara bin mahaifinsa yawon kiɗa da waƙa. Hakan ya sa idon Kassu ya buɗe dangane da salo da dabarun kiɗa da waƙa da kuma sanin wasu 'yantauri da mafarauta. Bayan rasuwar mahaifinsa sai Kassu Zurmi ya gaje shi a fagen kiɗa da waƙa, musamman na mafarauta da 'yantauri. Amma, shi Kassu ya shahara a fagen kiɗan farauta da na tauri da kuma kiɗan ɓarayi ta hanyar amfani da kayan kiɗa na kalangu. A sakamakon sharaharar Kassu, Sarki Zurmi ya naɗa shi Sarkin makaɗan maza na ƙasar Zurmi. Bayan kiɗa da waƙa kuma, Kassu yana taɓa noma. Kassu yana da kyakkyawar al'aƙa da makaɗan baka na Hausa a zamanin rayuwarsa. Hakan ya sa Alhaji (Dr.) Mamman Shata Katsina ya biya masa kujera ta aiki hajji, wanda ya je ya sauke farali. Haka kuma, Kassu Zurmi yana da abokan aiki guda uku waɗanda suke yi masa kiɗan kalangu, amma a tsari na rera waƙa, Makaɗa Kassu Zurmi makaɗin kaɗaita ne, wato shi kaɗai yake rera waƙoƙinsa ba a yi masa amshi. Allah ya yi wa Kassu Zurmi rasuwa a shekarar 1987 (Gusau, 2011:225-229 da Magaji, 2016:9-12 da Usman, 2011:154-156).

## 2.0 Yanayin Kimar Namiji Wajen Mace a Tsarin Zamantakewa a Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

Waƙoƙin Kassu Zurmi, waƙoƙi ne da suke tafiya tare da lura da yanayin zamantakewar al'umma. Hakan ya sa yakan yi wa al'umma nuni a kan yadda mata suke ƙimanta maza, musamman ma mafarauta da 'yantauri duk da yanayinsu na fatara. Mata ba su yi sai da maza kamar yadda su ma mazan haka. Kassu Zurmi yakan nuna yadda mata suke ba wa gwarzayen nasa ƙwarin guiwa ta hanyar nuna masu soyayya da ba su shawara da nuna gabata da rufa musu asiri da taimako ko tausayi.

### 2.1 Nuna Soyayya

Duk da yanayin 'yantauri da irin kallon da mutane suke yi musu na ƙasƙanci, mata sukan nuna musu soyayya. Wato suna gaskata maganar nan ta Hausawa da suke cewa, "soyayya gamon jini". Kassu ya nuna 'yantauri sukan sami soyayya daga wajen mata a bisa dalillai mabambata kamar jaruntaka ko ƙirar jiki da makamantansu. Misali:

Jagora : *'Yammata sun gane shi sun je mai,*
: *Anka ɗora wasoso,*
: *Ni wani Shayi ni ka jiɗe shi,*
: *A'a kina ƙarya na riga ki zaɓo shi,*
: Kamas su buga ga su nan cikin gebe,
: Na ce kak ku buga ya ishe ku jiɗawa.
Jagora : *Ɗaukash Shayaya munka sha daula,*
: *Mun sha ɗamnalutsa mun sha mai,*
: *Mun sha zabbi ga ɗan gidan Labbo,*
: *Nic ce ma 'yan yarana ku sha ahaha ce,*
: Tun da baya maishe ta.
(Magaji, 2016:68).

A wannan ɗan waƙa wanda Kassu ya kawo a cikin salo na raha, ya nuna yadda 'yanmata suke wasoson Shayi a wajen wani wasa inda kowace ta nuna tana son shi, sannan kuma, har da yin kari ko toshi da naman tattabara da zabbi da mai ga Shayi da abokansa da Kassu har da yaransa. Duk da cewa, 'yanmatan sun san Shayi ba shi da halin yin aure ko mayar da biki, wato ta hanyar yi musu kyauta ko toshi amma sun dage a kan son da suke yi masa. Kenan a iya cewa, wani lokaci so yana iya shiga da zarar an ga mutum ba tare da

tantancewa ba. Haka kuma, daga baya idan butaƙatar tantatncewar ta taso, akan yi janye ko ci gaba da soyayyar. Ga abin da Kassu ya ci gaba da cewa:

Jagora : Sai da za watcikkewa,
: *Kana Uwayen matanga sunka jawo ni*,
: *Ga ni ga 'yammantanga ga uwayensu,*
: *Mu kaɗai cikin azure,*
: *Kassu amana Allah ka ba mu labari,*
: *Nic ce, wane labari?*
: *Labarin Shayi ɗan gidan Labbo,*
:*'Yammata sun walwale baikonsu,*
: *Sun ce Shayaya shi ka ramkonsu*
: *Shi muka son ka ba mu labari,.*
: *In akwai gidan kirki,*
: *Nic ce yau kam dattijo kun ka maishe ni,*
: *Ya yi, ku koma ku shaida na Abu ɗan'uwa ne,*
:*Mutum kau ba ya shaidar ɗan'uwanshi ko hwada.*

Jagora : *Kassu amana Allah ka ba mu labari,*
: *Ni kau amana Allah kaɗai ka sha min kai,*
: *In na bi amana Allah ga na yi ɓatanci,*
: *Kuma in tuna ba ci amana Allah sabadda tatiri*,
: *Amma, hwa ku ba shi in kuna ba shi,*
: *Na Abu Shayi dai ɗa ne,*
: *Suka ce "Ba haka munka so ba ɗan yaro*
: *Ai mun san ɗa ne tun da anka haihe shi,*
: *Ba mu labari in akwai gidan kirki?*
Jagora : *Ni ce I gaskiyakka dattijo,*
: *Mutum kau ba za ya kai ɗiya tai ba,*
: *Gidan da ba abin kirki*,
: *Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,*
: *Sai ɗiyad dattijai kaɗai ka amren*,
: *Sha-yaya ɗan gidan Labbo, na Abu*
: *Tun da kowa amre shi ita ka ci she shi,*
: *Ta biya kuɗin garin Karen kyasko,*
: *Sannan ta yi mai abin ruhwa,*
: *Kana ta koma ta yi dabbalin abin ɗamri,*
: *Dattijo yat tashi yab buge riga yai cikin zaure.*
(Magaji, 2016:68-69).

A wannan ɗan waƙa da ya gabata, Kassu ya tabbatar da al'adar nan ta Hausawa ta tantance asali da kuma matsayin wanda za su aura wa 'yarsu. Wato su san yana da asali kuma yana da sana'ar da zai iya ɗaukar ɗawainiyar gidansa bayan an yi aure? Ta haka Kassu ya nanu an tambaye shi, amma ya ba su amsar cewa, Shayi ba shi da sana'ar yi. Fatara ta yi masa yawa ta yadda duk wanda ya ba shi aure to, shi zai ciyar da 'yarsa. Haka kuma, duk wadda ta aure Shayi ita za ta kula da kanta. Wannan dalili ya sa wannan dattijo ya ji Shayi ba mijin aure ba ne, saboda ba shi da halin riƙe mata. Muhimmim zance a nan shi ne, duk da la'akari da fatarar Shayi, sai da 'yanmatan nan suka nuna soyayyarsu gare shi a fili ta yadda har iyayensu suka shiga lamarin.

Ga wani misali:

Jagora : *Allah shi bi wa bukka buƙata uwargida,*
: *Allah shi bi wa bukka muradi uwargida,*
: *Koko Kuluwa tun da kun taimake ni,*
: *Kun dai ba ni sirirdi da mijinku ya ba ni doki,*
*(Waƙar Ɗanbaba Kore).*

A wannan ɗan waƙa, Kassu ya nuna yadda matan 'yantauri suke taimakonsu, musamman wajen kyauta. idan mijinsu ya yi wa makaɗi kyauta, to su ma sukan bayar da tasu kyautar gwargwadon hali. Kamar yadda a nan maigida ya bayar da kyautar doki su kuma matansa suka bayar da kyautar sirdi. Wannan ke nuna a kullum macen kirki tana tare da mijinta wajen aikin alheri.

## 2.2 Bayar da Shawara

A cikin ƙunshiyar zamantakewa tsakanin miji da mata ko 'yan'uwa da abokan arziki akwai bayar da shawara, musamman ma idan akwai soyayya. Shawarwari sukan amfani wanda aka baiwa, idan sun kasance kyawawa. Ga misali:

Jagora : *Labbo yac ce ƙaton gidan na banza ne,*
: *Komi yab biɗa na mata ne,*
*: Dum mata sun bi Iro sun koɗe,*
*: 'Yaƙ ƙamnatai tana yi mai wazu, ɗ2*
*: La'anannen ba ya jin batun ƙannai,*
*: La'anannen ba ya jin ba,*
*: Tana hwaɗin,*
*: Tana hwaɗi Shayi ga ka dai da ƙarhin, Shayi ga ka dai danka,*
*: Na Abu hak ka lalace tsohuwa ta cishe ka. ɗ2*
*(Kassu Zurmi, Waƙar Ɗanbaba Kore).*

A wannan ɗa Kassu ya nuna yadda ƙanwar Labbo take shawartar yayanta domin ya tsaya da ƙafarsa kuma ya san abin da ya kamata ya riƙa yi da abin da ya samu ko ya kula da su, ya kare musu mutuncinsu. Amma Labbo ya ji wannan shawara, sai dai duk abin da ya samu mata yake ba. Hakan ya sa bai amfana wa kansa komai ba balantana ya taimakin ƙannansa. A nan ma an fito da kyakkyawar alaƙar mata da maza, wanda wannan dalili ne ya hana Labbo amfana wa kansa da 'yan'uwansa komai. Ma'ana idan danagantakar namiji da mace ta kasance ba ta gaskiya ba, to mata sukan hana wasu mazan amfana wa kansu komai. To sai dai ƙanwarsa ta ɗauke nauyin da ya rataya a wuyanta na ba shi shawarar da ta dace.

## 2.3 Ɗaukar Ɗawainiya

Idan mace tana son namiji, ba ta damuwa wajen yin hidima ko wata ɗawainiya da ta wajaba a kansa ta hanyar amfani da dukiyarta. Wannan ƙauna takan rufe wa mace idon ganin laifin masoyi. Idan ya yi sa'a tana da hali da zuciya, sai ɗawainiyar ta koma kanta. Ga misalin irin haka kamar yadda Kassu ya kawo:

Jagora : *Mata ta haihu babu kayan barka,*
: *Ba gishiri, ba kanwa ba tsaba ba yaji,*

: *Sannan ba a ba shi bashi*
: *Kuma ba a ba shi kyauta, kuma ba mai ba shi rance.*
Jagora : *Shiririta ta yi maigida ba ƙwara,*
: *Bature ga ka da ƙwazon ciki babu rago,*
*:Na gode Imdai mai ɗauki nai,*
*: Na gode Imdai matak kaskona,*
*: Ita tak kira ni tam man doki, kuma itat tai surdi,*
Jagora *: Tay yi tuwo tab ba ni,*
: *Mutane maigida yana tule ko kwabo ya buwaye.*
*(Kassu, Waƙar Bature).*

A wannan ɗa Kassu ya fito da yanayin soyayya a tsakanin ʻyantauri da matansu, ta hanyar fito da yadda mata suke nuna gabata wajen ɗauke wani nauyi da yake a kan maigida, musamman a lokacin da ba shi da halin sauke wannan nauyi da ya ɗoru a kansa. Wataƙila Kassu ya kawo wannan misalin ne ganin yadda ake danganta ʻyantauri da tsiya ko fatara. Amma abin jan hankali a nan shi ne irin kulawar da ʻyantauri suke samu daga matansu musamman na ɗauke ɗawainiyar da ba tasu ba. Kassu ya kawo yadda Imdai matar Bature ta yi hidimar suna, sannan kuma har ta yi masa (Kassun) kyautar doki da sirdi kuma ta ba shi abinci. Kenan a iya cewa, zama ya yi daɗi har wannan mata ba ta son jama'a su ga kasawar mijinta saboda soyayya. Haka kuma ba ta son makaɗinsa (Kassu) ya yayata shi, ta yi ƙoƙarin rufe masa baki da kyautar doki da abinci.

## 2.4 Rufa Asiri

Zamantakewa tsakanin maza da mata ko miji da mata akwai rufin asiri, musamman idan akwai kyakkywar dangantaka. ʻYantauri yawanci sukan nemi rufin asiri daga wajen matansu kafin su nema a wajen wasu na daban. Ga ʻyantauri, irin wannan rufin asiri ya shafi wata buƙuta ko a kan wata rigima ko wata ta'asa da suka yi ko suka ɗauko. Misali inda Kassu yake cewa:

Jagora : *Ni nac ce duk abin da kas samo, kawo a cikama saura,*
: *Yac ce abin da ban-kumya, amma bari im ɗan ranto,*
: *Ya koma ya ranto ya isa gun mata nai,*
: *Yaz zo gun ƙane nai,*
: *Ya kai ma maƙwabta kuka.*
(Kassu, Waƙar Ɗanbuzu).

A wannan ɗan waƙa Kassu ya nuna yadda aka yi wa Ɗanbuzu alƙawali cewa ya kawo wani abu, wato kuɗi ko da kaɗan ne za a cika mai saura, amma babu. Haka ya sa ya fara zuwa wajen matansa don fita kunya ya ranto kafin ya tafi wajen ƙanensa da kuma maƙwabta. Wato tunanin fara tuntuɓar mata don fita kunya ya tabbatar da an saba rufa mai asiri idan irin haka ta taso.

## 2.5 Nuna Tausayi/ Taimako

Mata, mutane ne masu nuna tausayi musamman ga wanda suke so don su ceci rayuwarsa daga salwanta ko tabka mummunan aiki. Wani lokacin idan ba su nuna tausayin ba, to abin yakan shafe su da kuma ʻya'yansu. Ga misali:

Jagora : *Sai nij ji mata na kuka,*
: *Don Allah Saraki zaburo za ya hita*,

: *Don Allah Saraki zaburo za kay ya tahi,*
Jagora : *Yara ashe Saraki ba ya taƙama*,
: *Ya ga bila'i za shi hwaɗa ma gari,*
: *Sai nag ga Saraki an hito ba rawani,*
: *Nij ji yana hwaɗin ku taushe mani shi,*
: *Ku kame mani shi ɗ²,*
: *Yas sa haɓe sunka kame mani shi.*
(Gusau, 2009:372).

A nan Kassu ya nuna yadda mata suka nuna tausayi ta hanyar neman taimakon Saraki a lokaci da tsiya ta motsa wa Nomau zai je ya yi ɓarna. Saboda wajen yin ɓarnan nan, zai iya shiga matsala ya yi abin da za a ɗaure shi ko kuma reshe ya juye da mujiya. Hakan ya sa mata suka nemi Saraki ya taimaka, ya kira mutanen gari musmaman majiya ƙarfi su kama Nomau su hana shi tafiya wajen aikata ɓarnar da yake son aikatawa.

**3.0 Kammalwa**

A wannan nazari an yi sharhi a kan yanayin dangantaka tsakanin maza da mata, musamman jarumai, wato 'yantauri da mafarauta a tsarin zamantakewar Hausawa. An fito da yanayin nuna soyayya da bayar da shawara da ɗaukar ɗawainiya da rufin asiri da kuma nuna tausayi. Haka kuma an fahimci Kussu yakan lura da yanayin zamantakewar al'ummar Hausawa, musamman jarumansa da kuma matansu da sauran mata masu son su ko waɗanda suke so. Wato bai tsaya ga zugi ko yabo ko kuma bayar da labarin accakwamar da aka yi da su ba. Kassu ya fahimci wasu al'adu da suka shafi dabarun inganta zamanatakewa ta hanyar yi wa al'umman hannunka-mai-sanda don inganta da kyautata dangantaka a tsakanin al'umma. Misali kamar yadda aka tambayi Kussu dangane da Shayi, inda ya faɗi gaskiyar cewa, ba shi da abin yi, wato ba zai iya riƙe mata ba. Wannan dalili ya sa wannan dattijo ya janye maganar aure tsakanin shi da 'yarsa. Wannan daɗaɗɗiyar al'adar ce ta Hausawa ta yin bincike a kan wanda zai auri 'yarsu domin tabbatar da asalinsa da kuma sana'arsa. Wato yana da halin riƙe mata idan an aura masa ko ko a'a? Hausawa a harkar aure baya ga asali, sun fi ba sana'a ko abin yi fifiko.

Haka kuma, a wannan nazari an lura akwai dalilai da dama da suke ƙara inganta danganataka tsakanin maza da kuma mata ('yantauri da mafarauta da matansu). Misalin waɗannan dalilai su ne jarunta da siffa ko yanayin jiki (ƙarfi) da iya ma'amalar aure. A wurin matan 'yantauri, rashi kuɗi ko wadata ko kantar fatara ba su da tasiri wajen gurɓata danganataka tsakaninsu da matansu. Shi ya sa jaruman suke samun haɗin kan matansu ta fuskar nuna soyayya da taimako da rufin asiri da bayar da shawara da ɗaukar ɗawainiya.

**Manazarata**

Bunza, A.M. (2009). *Narambaɗa*. Lagos: Ibrash Islamic Publishers Centre Limited.

Bunza, A.M. (2014). *In Baka san Gari ba Saurari Daka: Muryar Nazari Cikin Tafashen Gambo.* Cairo: Elkods Printing House.

Funtua, A.I. (2015). Nazari a Kan Waƙoƙin Makaɗan Baka na Hausa a Jihar Katsina Daga 1978 Zuwa 2012. Kundin Digiri na Uku (Ph.D Thesis) . Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero, Kano.

Gusau, S.M. (1988). Waƙoƙin Makaɗan fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu. Kundin Digiri na uku (PhD Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Gusau, S.M. (2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano:Benchmark PublishersLimited.

Gusau, S.M. (2008). *Waƙoƙin Baka a Kasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu.* Kano:Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). *Diwanin Waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa.* Kano: Century Reseach and Publishing Limited.

Gusau, S.M.(2011[a]). *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2011[b]). "Tarihi da Hanyar Nazarin Waƙar Baka Bahaushiya a Taƙaice" in Funtuwa, A.I. da Gusau, S.M. (Editoci) *Waƙoƙin Baka na Hausa.* Kano: Century Reseach and Publishing Limited.

Gusau, S.M (2014). *Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa oral song)*. Kano:Professional Inaugural Lecture, Series NO.14. Jami'ar Bayero.

Kaura, H.L. (2017). Salon Zayyana (Hotancin Zucci) A Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sokoto.

Lawal, N. da Tahir, M.R. (2025). Falsafar Waƙoƙin Baka a kan Dangantakar Shugabanci da Cigaban Kasa. *Zamafara Internatoinal Journal of Humanities, Vol. 3 (1).* 111-120. www.doi.org/10.36349/zamijoh.2025.ɓ03i01.012. Zamafara: Faculty of Humanities, Federal Uniɓersity, Gusau.

Magaji, A. (1980). Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa Kundin Digiri na Ɗaya (B.A. Dissertation). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Magaji, A. (2016). Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa. Ibadan: Specrum Books Limited.

Satatima, I.G. (2009). Waƙoƙi Baka na Ɗarsashin Zuciya: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu" Kundin Digiri na uku (PhD Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Sulaiman, I.I (1983). Waƙoƙin Ɓarayi. Kundin Digiri na uku (B.A. Dissertation). Sashen Harsunan Afirka da Al'adu. Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Usman, H.S. (2011). Tarihi da Waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi, in Funtuwa, A.I. da Gusau, S.M. (Editoci) *Waƙoƙin Baka na Hausa.* Kano: Century Reseach and Publishing Limited.

Yahya, A.B. (1997). *Jigon Nazarin Waƙa*. Kaduna: Fisbas Media Services.

Yahya, A.B. (2001). *Salo Asirin Waƙa.* Kaduna: Fisbas Media Services.